## ABOUT CITAD

CITAD (www.citad.org)
Is A Capacity Building Civil Society Organization
Whose Activities Covers Research, Advocacy,
Training And Publicity In All Areas Of Icts.
Its Vision Is; A Knowledge-based Democratic Society
Free Of Hunger While Its
Mission Is; Using ICTs To Empower Citizens For
A Just And Knowledge-based Society
That Is Anchored On Sustainable
And Balanced Development.

**MAIN OFFICE:**
3rd Floor, NISTF Building, No.1A, Social
Insurance Road, Behind Trade Fair Complex,
Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 0800-68078282, 080-54362931, 070-33427467 •
E-mail: info@citad.org, Citadev@gmail.com, citad4peace@citad.org,
Website: www.citad.org, www.citad4peace.org.ng

**BAUCHI OFFICE:**
NUJ Secretariat, Opposite Reinsurance House,
Ahmadu Bello Way, Bauchi State.
GSM: 08064867312

**CITAD**.....*A Knowledge-Based Democratic Society Free of Hunger*

*Tsarawar*
Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)
Tare Da
Gudummawar ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)

# KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN UNGUWAR YAKASAI



**CENTRE FOR INFORMATION TECHNOLOGY AND DEVELOPMENT**

# KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN UNGUWAR YAKASAI

*Tsarawar*

**Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)**
**Tare Da**
**Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)**

CITAD actionaid UKaid from the British people





## ABUBUWAN DA KE CIKI


Shafin Farko....................i
Jadawali....................ii
Godiya....................1
Gabatarwa....................2
Manufa....................3
Hanyoyin Da Aka Yi Amfani Da Su....................3
Tsarin Da Aka Yi Amfani Da Shi....................3/4
Cikakken Bayani Game Da Yakasai....................4/6
Tarihin Unguwar Yakasai....................6/8
Taswirar Unguwar Yakasai....................8/9
Yanayin Zamantakewa....................9/10
Lafiya....................10
Ilimi....................10/12
Juyawar Yanayi....................13
Jadawalin Juyawar Yanayi Na Tsahon Shekara....................13/14
Kadarori....................14
Tantance Matsalolin Da Ke Addabar Yakasai....................15/17
Tantance Haƙƙoƙin Mata....................18/20
Take Haƙƙoƙin Ɗan Adam....................21/22
Kalubalen Da Ke Fuskantar Unguwar Yakasai A Halin Yanzu....................22/23
Sassauƙar Hanyar Jera Matsaloli....................23/24
Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli....................25/26
Kungiyoyi Da Mutanen Da Zasu Iya Tallafawa Unguwar Yakasai (masu Iko Da Hukumomi)....................27/28
Tantance Yanayin Karfin Iko (Nazari Kan Waɗanda Keda Iko)....................28/31
Tantance Hanyoyin Samun Bayanai....................32
Tsarin Da Aka Shirya Gudanarwa Na Al`Umar Unguwar Yakasai....................33
Hotunan Da Akayi Amfani Dasu Wajen Sassauƙar Hanyar Jera Matsaloli....................34

# GODIYA

Wallafawar wannan littafi yasamu yiwuwane tareda tallafi daga Sashin Kula da Cigaba na ƙasa da ƙasa na Gwamnatin Birtaniyya (DFID ta hannun ƙungiyar ActionAid Nigeria (AAN). Dole ne a yabawa wannan Cibiya ta ActionAid saboda jajircewa ta wajen Bunƙasa Demokuraɗiyya ta hanyar wayar da Jama'a su fahimci Demokuraɗiya.

Muna godiya ta musamman ga Shugaban Cibiyar Fasahar Sadarwa da Ci gaban Al'umma (CITAD), Y.Z. Ya'u domin kasancewarsa jigo wanda ya bada gudummawa ga kammaluwar wannan Littafi.

Godiyar mu bazata cikaba sai mun yaba da Kyakkyawar fahimta da hadin kai da ma'aikatan CITAD. Haka kuma mun yabawa da ƙoƙari da himmar Malam Ahmad AbdullahiYakasai, da Isyaku Garba' da Abubakar Auyo da Mukhtar Sulaiman Umar da Abdullahi Jido da Harira Abdulrahman wanda suka hana kansu hutu domin tabbatar da kammaluwar wannan Kundi.

Muna miƙa cikakkiyar godiyarmu ga 'Yan kwamitin aiwatar da kundin wannan Unguwa ta Yakasai da Mai Unguwa da kuma dukkannin waɗan da suka tallafa wajen gudanar da tsarin shirin wannan kundi, babu shakka zai ingan ta shirin nan gaba.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN UNGUWAR YAKASAI 2016

# GABATARWA

Wannan kundi na cigaban wannan unguwa yana ɗauke da gabaɗayan bayanai filla-filla da kuma taƙaitattu abubuwan da suka shafi unguwar Yakasai dake Karamar Hukumar Birni da Kewaye a jihar Kano a tarayyar Najeriya. Wannan kundi zai zama wani makami na yin wuƙar-ƙugu wajen tabbatar da gaskiyar al'amura ga jama'ar Yakasai. Kundin ya yi cikakken bayanin unguwar da mutanenta da kuma albarkatun ƙasa da Allah Ya huwace mata. An tattaro waɗannan bayanai ne daga wajen wasu keɓantattun mutane mazauna unguwar ta hanyar yin amfani da tsarin waiwaye adon tafiya domin yin bitar abubuwan da suka gudana da kuma tsarin nan na Action Aid wanda ke bai wa kowa damar bayar da gudummawa don faɗakar da mutane sanin muhimmancin kowa ya shiga a dama da shi a al'amuran zaɓe wanda aka fi sani da (SCEEP).

Tsarin zai zama wani ginshiƙi na aiki tare da wasu unguwanni a ƙoƙarin saita al'umma kan gwadaben da za su rinƙa bibiyar abubuwan da gwamnatoci da wakilansu ke gudanarwa. Haka kuma, wannan kundin zai samar da wata kafa ta yin aiki tare tsakanin al'ummar unguwar da waɗanda suka zaɓa zuwa matakai daban-daban. An samar da kundin ne ta bin managartan tsare-tsare da wannan ƙungiya ta yi a baya, aka tattaro ƙwararru suka yi aiki ƙarƙashin inuwa ɗaya.

Hanyar amfani da tsarin waiwaye adon tafiya na yin amfani da cikakken bincike kamar binciko dangantakar mahukunta da haƙƙoƙin al'umma musamman mata da gano abubuwan da ke yi wa unguwar barazana da binciko ƙungiyoyi da mutanen da za su iya tallafawa da fahimtar hanyoyin sadarwa da al'ummar unguwar ke amfani da su da kuma matsalolin da suke ci musu tuwo a ƙwarya.

`Domin cimma nasara abubuwan da aka ambata a sama, Action Aid ta aiwatar da tsarin waiwaye adon tafiya a unguwar. Ta amfani da sassa bakwai na tsarin tantancewar bayanan da aka tattara domin su zama ginshiƙai na ƙarfafa gwiwa wanda zai ciyar da unguwar gaba yadda ake buƙata.

MANUFA

Manyan manufofin wannan kundi su ne kamar haka:

- Gano tare da adana al'amuran da suka shafi unguwar Yakasai tare da fitar da wani tsari na shigo da al'ummar yankin don yin aiki tare.
- Zaburar da al'umma wajen neman abubuwan cigaban unguwar daga wakilansu a ɓangarori daban-daban.
- Tallata ƙwarewa da ilimi da kuma abubuwa da unguwar Yakasai ke fatan samu a dunƙule domin samun sauƙin bibiya.

HANYOYIN DA AKA YI AMFANI DA SU

Hanyoyin da aka bi wajen aiwatar da aikin sun haɗa da:

- Tattaunawa tun a karon fari tsakanin dattawan Yakasai da CITAD.
- Ziyarce-Ziyarce: An ziyarci wurare daban-daban tare da ganawa da mutanen unguwana tsawon kwanaki domin samun cikakkun bayanai na ɓangarorin nan bakwai na Reflection Action.
- Taron tantancewa da rubuta rahoton abubuwan da aka gano.

TSARIN DA AKA YI AMFANI DA SHI

An yi amfani da abubuwa daban-daban wajen tantance ɓangarori nanbakwai na waiwaye adon tafiya wato Reflection Action.

An yi amfani da taswira wajen binciko matsalolin da ke addabar unguwar.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN UNGUWAR YAKASAI 2016

An yi amfani da jerin gwanon Haƙƙoƙi Ɗan Adam wajen gano haƙƙoƙin al'ummar Yakasai.

Jera abubuwa mafi sauƙi ya taimaka wajen tsara al'amuran da suka fi muhimmanci bi da bi waɗanda al'ummar unguwar suka gano.

An yi amfani da bishiyar-matsaloli domin fahimtar abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu da kuma tattaunawa mai zurfi a kansu.

An yi amfani da salon tantance cibiyoyi da mutanen da za su iyabayar da tallafi domin gano waɗanda za su iya hoɓɓasa kuma suke da ikon kawo canji ga abubuwan da unguwar ke buƙata.

An yi amfani da tsarin zane naVenn domin a tantance matakin tasirin da cibiyoyi da mutanen da za su iya taimakawa da alaƙarsu da unguwar.

An yi amfani da salon yanar-gizo wajen tantance haƙƙin mata.

Tsarin tantance matsaloli ya fitar da abubuwa daban-daban da ka iya cutar da unguwar.

Zanen hanyoyin sadarwa ya tantance hanyoyin da al'ummar unguwar ke isar da saƙonni tsakaninsu da sauran unguwanni da waɗanda za su iya bayar da gudummawa. A ƙoƙarin aiwatar da tantance abubuwa daban-daban, an tattauna da kowa da kowa, an tattauna a ƙungiyance don a yi tambayoyi da kuma yin bincike mai zurfi domin a samu tantancewa mai inganci.

# CIKAKKEN BAYANI GAME DA UNGUWAR YAKASAI

Sunan Unguwa: Yakasai
Karamar Hukuma: Municipal
Jiha: Kano
Adadin Al'umma: 28,039 (Maza 13,100, Mata 14,939)

## AJUJUWAN SHEKARUN AL'UMMAR UNGUWAR

| AJUJUWAN SHEKARU | KIYASI |
|---|---|
| Shekara 0 zuwa 5: | 1,600 |
| Shekara 6 zuwa 10: | 1,000 |
| Shekara 11 zuwa 18: | 7,000 |
| Shekara 19 zuwa 30: | 6,200 |
| Shekara 31 zuwa 40: | 4,100 |
| Shekara 41 zuwa 50: | 3,000 |
| Shekara 51 zuwa 60: | 1,000 |
| Shekara 61 zuwa 70: | 4,000 |
| Shekara 70 zuwa sama: | 139 |
| **JUMULLA** | **28,039** |

Sana'oi /Aikin yi:Sana'r Gini (Birkilanci), Adon Masarautu (Dagi), Ɗinki, Kananan 'Yan Kasuwa da Ma'aikatan Gwamnati.
Kuɗaɗen da ke shigowa/Kuɗaɗen da ake kashewa
Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a shekara: **₦450, 000**
Matsakaicin abin mutum yake kashewa a shekara: **₦450, 000**3
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake samu a Shekara: **₦600, 000**
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake kashewa a Shekara: **₦600, 000**

## LAFIYA

Ɗakin Shan Magani: Unguwar nada Ɗakunan Shan Magani guda 2 mallakin 'yan unguwa, Ɗakin Shan Maganin nada tazarar 0.5km cikin unguwar. Gashikuma unguwar tayi maƙwotaka da babban asibitin Jiha.





## ILIMI

| | | | |
|---|---|---|---|
| Adadin yaran da suka shiga makaranta a halin yanzu: | Adadin yara maza: 900 | Adadin yara mata: 1210 | Adadin 'yan ƙasa da shekara 5: 2031 |
| | Adadin yara 'yan shekaru 6 zuwa 10: | Adadin 'yan shekaru 11 zuwa 15: baƙiyasi | Adadin 'yan shekaru 16 zuwa 20 (idan ana buƙata): ba |

| | |
|---|---|
| Adadin waɗanda suka kammala firamare a unguwar: 3500 | Adadin Maza:2450 |
| | Adadin Mata: 1050 |
| Adadin waɗanda suka kammala sakandare a unguwar: **6635** | Adadin Maza: **4400** |
| | Adadin Mata: 2235 |
| Adadin waɗanda suka kammala makarantar gaba da sakandare a unguwar: 8500 | Adadin Maza: **5000** |
| | Adadin Mata: **5000** |
| Adadin waɗanda ba su taɓa zuwa makaranta ba: **40** | Adadin Maza:15 |
| | Adadin Mata: 25 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa makarantar firamare: **20** | Adadin Maza: 13 |
| | Adadin Mata: 07 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa makarantar sakandire: Dalilin da ya shafi jahilci ko kuma dalilin faduwar jarabawar kwalafayin **102** | Adadin Maza: **32** |
| | Adadin Mata: 70 |

Masu buƙata ta musamman (PWDs):sama da 67




## TARIHIN UNGUWAR YAKASAI

Yakasai ɗaya ce daga cikin mashahuran unguwanni a Karamar Hukumar Birni ta jihar Kano. Kamar yadda waɗansu suke cewa, an samo sunan unguwar ne daga al'ummar Kwararrafa ta Wukari (yankin jihar Taraba ta yanzu)waɗanda suka zo Kano domin farauta. Daga zuwansu sai suka sauka a inda unguwar Yakasai take a yanzu. A wancan lokacin wurin jeji ne duk da cewa wurin na cikin ganuwa. Duk lokacin da suka tafi farautar sukan dawo wannan wajen (Yakasai) inda suke gyatta naman farautar da sukayi.Lokacin da suka buƙaci komawa gida, sai aji suna cewa 'YAKASAI' wadda a harshensu take nufin 'sai mun dawo' wannan shi yake nuna cewa suna jin daɗin zaman wajen. Bayan mutanen Kwararrafa sun daina zuwa garin Kano, wasu 'ya'yan sarki sun zauna a wannan gurin tare da bayinsu da wasu mutane da suka ƙwarai wajen sana'ar gini.Inda suka bunƙasa

gurin aka kuma cigaba da kiranwannan guri da suna 'YAKASAI'.Wannan lamari ya faru ne tun lokacin mulkin Sarkin Kano Bello Ɗan Dabo. Haka kuma wannan na daga cikin dalilin da yasa har yanzu unguwar Yakasai ke da shahararrun mutane da suka ƙwarai wajen sana'ar gini na gargajiya masana wajen tsanen ƙawa na gini da rufin ɗaki na gargajiya da aka fi sani da suna 'Dauringuga'. Daga cikin mazauna gurin na asali akwai mutanen Damagaran (cikin Jamhuriyar Nijar ta yanzu). Unguwar Yakasai na kewaye da unguwanni da dama kamar unguwar Kankarofi, Durumin Zungura, Kofar Nassarawa, Kofar Mata, Unguwar Gini, Kurmawa, Indabawa da unguwar Gwangwazo. Yakasai ta haɗa ma'aikatan gwamnati da dama, ƙananan 'yan kasuwa, maɗinka, magina, 'yan kwangila da masana ilimin addini da ilimin boko. A gargajiyance, unguwar Yakasai na ƙarƙashin shugabancin masu unguwanni guda 2. Mai unguwar Yakasai 'A' da Mai unguwar Yakasai 'B' waɗanda ayyukan ƙungiyar Yakasai Zumunta ke tallafawa domin cigaban unguwar. Duk da daɗaɗɗen tarihin wannan unguwa, unguwar na fama da matsalolin 'yan shaye-shaye dana 'yan daba da rashin zauren bayar da shawarwari da kulawa ta musamman da matsalar rashin aikin yi.

SANA'OI /AIKIN YI: Dangani da sana'a, sama da kashi 70% na al'ummar wannan unguwa ma'aikatan gwamnati ne dake aiki a ma'aikatu daban-daban na gwamnati. Sauran al'ummar kuwa ƙanana da matsakaitan yan kasuwa ne, sai masu sana'ar hannu kamar Birkiloli, masu zanen ginin masarautu da sauransu.

ABUBUWAN MORE RAYUWA: Unguwar Yakasai nada ruwan fanfo, sai wasu guraren a unguwar na shan wahala wajen samun tsaftaceccen ruwan sha, saboda wasu lokutan jama'a kanyi wattani babu ruwa. Saboda haka ne mutane ke amfani da ruwan rijiya dana tuƙa-tuƙa wajen ɗiban ruwa.





ILIMI: Dangani da ilimi, akwai masu tarin ilimi da yawa a unguwar Yakasai, ilimin addini danaboko. Unguwar nada makarantun firamare guda 21 na sakandire guda 8.

LAFIYA: Akwai Ɗakunan Shan Magani guda 2 a unguwar wanda 'yan unguwar ke zuwa domin duba lafiyarsu da abubuwan da suka shafi ɗigon riga kafin maganin cutar shan inna (N.P.I). Tazarar 0.5km ne tsakanin ɗakunan shan maganin da unguwar. Adadin ma'aikata 21 ke akwai a ɗakunan shan maganin 5 maza 16 mata.Kamar yadda mazauna wannan unguwa suka faɗa,ko da yaushe akan sami ma'aikatan lafiyar a ɗakunan shan maganin, haka kuma idan annoba ta ɓarke akan sanar da hukumar data dace ta hannun Mai unguwa da ma'aikatan lafiyar unguwar. Kananan yara yan ƙasa da shekara biyar su suka fi saurin kamuwa da cututtuka. Yawanci mata masu juna biyu kan haihu a ɗakunan shan maganin, ƙalilan daga cikin matan kan haihu a gida. Idan haihuwar tazo da matsala, matankan tafi zuwa babban asibitin jiha don haihuwa a can wanda ke kusa da unguwar. Sai dai cewa an ɗan sami cigaba kaɗan akan abubuwan da suka shafi lafiya a unguwar shekaru 3 baya musamman yadda ake bada magani kyauta da taimakon da'yan sa kai jami'an lafiya ƙwararru dake zaune a unguwar ke bayarwa (Likitoci).

TASWIRAR UNGUWAR YAKASAI

Samar da taswirar ya soma ne da tattaki cikin unguwar.Al`umar unguwar ne suka gudanar da tattakin wajen zana tasawirar unguwar tasu, domin gano albarkatun ƙasar da Allah ya horewar unguwar, ƙalubalen dake fuskantar unguwar da matsalolinsu ta hanyar tattaunawa don samin cikakken bayanin unguwar. Yayin samar da taswirar ba a gano waɗansu albarkatun ƙasa ba sai dai bishiyoyi da sauran ababan more rayuwa.



Yunƙurin samar da taswirar unguwar Yakasai



YANAYIN ZAMANTAKEWA

Unguwar Yakasai na cikin Ƙaramar Hukumar Birni wadda take da yawan al'umma da yakai adadin mutane 28,039 (13,100 maza da 14,939 mata). Babu wata ƙididdiga da ta nuna rabe-raben jagoranci a tsakanin iyalai.

Adadin yara tsakanain shekaru 0-5 su suka fi yawa a wannan unguwa (duba ajujuwan al'ummar unguwar domin ƙarin bayani)

Bugu da ƙari, mutanen wannan unguwa yawancinsu manoma ne da ƙananan yan kasuwa. Manoman kan noma gero, dawa, rogo da kayan gwari. Matsakaicin abin da ke shigowa mutum magidanci a shekara a shi ne

N153,000. Haka kuma matsakaicin abin da Mutum magidanci ke kashewa a kullum yakai N 300. Mazauna wannan unguwa kan kashe yawancin abin da suke samu a harkokin yau da kullum saboda noman kayan miyar da suke.



Akwai ƙalilan ɗin ma'aikata da ke samun N1800 da N250 a kullum.




## LAFIYA

Unguwar nada Ɗakunan Shan Magani guda biyu waɗanda ke da kayayyakin aiki da ƙwararrun ma'aikatan lafiya guda 21, 5 maza 16 kuma mata don kulawa da masu Juna biyu yayin haihuwa.Unguwar bata taɓa fuskantar wata annobar cututtuka ba kamar zazzaɓin maleriya, tayfod da gudawa. Ɗakunan shan maganin kan karɓo magunguna domin tunkarar waɗannan cututtuka. Akwai ƙalilan ɗin Ungozomomi na gargajiya a unguwar. A lokacin tattaunawar an bayyana cewa akwai buƙatar ɗaga darajar ɗakunan shan maganin dake unguwar saboda idan haihuwa tazo da tangarɗa kai tsaye sai an tafi babban asibitin ƙwararru na Murtala Muhammad.



## ILIMI

Unguwar Yakasai nada makarantar firamare guda 21 da makarantun sakandire guda 8. Ajujuwa da banɗakunan Makarantun na cikin kyakykyawan yanayi sai dai akwai buƙatar kujerun zama a ajujuwan da ofisoshin malamai.

Bugu da ƙari, makarantun al'ummar unguwar Yakasai nada adadin ɗalibai 7,500 2800 daga ciki mata sannan 3700 maza.A wannan unguwa, alƙalumman daukan yara a makaranta ya nuna cewa ana bada muhimmanci korai da gaske wajen ɗaukan yara mata a makaranta.Akwai cigaba idan an kwatanta da baya inda yara mata ke fuskantar auren wuri a wannan unguwa. Haka kuma mata 25 daga cikin 40 basu taɓa halartar makarantar boko ba. Wannan shi yake nuna cewar anfi bada muhimmanci wajen ɗaukar yara mata a makaranta a halin yanzu, wanda hakan ba koyaushe yake faruwa ba.

Anyi amfani da Shirin bunƙasa damar samun ilimi PRS domin tantance inganci ilimi a unguwar Yakasai. Shirin bunƙasa damar samun ilimi PRS ya fayyace haƙƙoƙi guda 10 da aka samu daga dokokin ƙasa misali anyi amfani da kundin tsarin mulkin ƙasa da tarukan kare haƙin dan adam wajen tantance ingancin ilimi a unguwar.

Babbar manifar wannan shiri na PRS shi ne shigar da yan ƙasa cikin tsarin bunƙasa ilimi. Anyi amfani da kundin wajen tantance mizanin fahimtar damar samun ilimi musamman ta fuskar al`umar wannan unguwa susan cewar damar suce.Tare da mizani mai lamba 1 mafi ƙaranci da lamba 5 mafi girma. Jadawalin da ke tafe yayi ƙarin haske

## YARJEJENIYAR BUNKASA DAMAR SAMUN ILIMI PRS TA UNGUWAR YAKASAI

| LAMBA | HAKKOKI (SHIRIN BUNKASA DAMAR SAMUN ILIMI PRS NA UNGUWARYAKASAI) | TANTACEWA (1 MAFI KARANCI, 5 MAFI GIRMA) |
|---|---|---|
| 1. | Haƙƙoƙin samun kyakkyawan ilimi kuma kyauta | 2 |
| 2. | Haƙƙoƙin rashin nuna wariya | 1 |
| 3. | Haƙƙoƙin samar da isassun kayayyakin more rayuwa | 5 |
| 4. | Haƙƙoƙin samara da ƙwararrun malamai | 4 |
| 5. | Haƙƙoƙin samar da wajen zama mara haɗari | 4 |
| 6. | Haƙƙoƙin samar da tsarin koyarwar da ya dace (manhaja) | 1 |
| 7. | Haƙƙoƙin sanin 'yancin kai | 3 |
| 8. | Haƙƙoƙin a dama da mutum a wajen ɗaukar mataki | 1 |
| 9. | Haƙƙoƙin samar da makarantu ingantattu marasa ƙunbiya-ƙunbiya | 1 |
| 10. | Haƙƙoƙin samar da ingantacciyar koyarwa | 3 |

KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN UNGUWAR YAKASAI 2016





## JUYAWAR YANAYI

Unguwar Yakasai tana da yanayi iri biyu, rani da damina.Ana samun yanayin rani ne daga watan Nuwamba zuwa watan Afrilu.Damina kuwa tana farawa daga watan Mayu, inda ruwa yakan kankama tsakanin Agusta da Satumba. Jihar Kano kacokan ta fi samun yanayin zafi da yawa, ruwan sama(watau damina) yawanci akan same shi ne a watannin Mayu da Yuni da Yuli da Agusta da kuma Satumba. Kano na samun rani a watannin Janairu da Fabrairu da Maris. Akan samu matsakaicin zafi a watan Maris da Afrilu, yayin da sanyi ya fi tsananta a watan Nuwamba.Agusta da Satumba sune watannin da aka fi samun ruwan sama, haka kuma Janairu ne watan da rani ya fi tsamari. Ayyukan noma a unguwar ba shi da yawa sosai saidai ma'aikata da ƙananan kasuwanci.Mutanen wannan unguwa ta Yakasaikan shirya domin ayyukan noma a watannin Maris da Afrilu. Jadawalin da ke biye yana nuna yadda yanayin ya karkasu da kuma yadda ayyukan suke gudana a tsakanin waɗannan lokutan.

### YANAYIN UNGUWAR UNGUWAR YAKASAI A TSAWON SHEKARA

| Abubuwan da ake yi | Janairu | Fabrairu | Maris | Afrilu | Mayu | Yuni | Yuli | Agusta | Satumba | Oktoba | Nuwamba | Disamba |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Kasuwanci | M | | | VH | | | | H | | | M | |
| 1.Ɗinki | M | M | M | M | H | H | H | L | L | L | L | H |
| 2.Maleriya | L | H | H | H | H | H | L | L | L | L | L | H |
| 3.Kwalara | L | H | H | H | H | H | L | L | L | L | L | H |

Karin Haske: VHSama da Gaske H Sama M Matsakaici L Kasa VL Kasa Sosai








Yanayin Unguwar Unguwar Yakasai a Tsawon Shekara

Tsakanin watan Fabrairu da Maris, Maɗinka a unguwar Yakasai basu da ayyuka sosai kamar a watannin Mayu, Yuni da Yuli lokacin da suke cikin ayyuka mutuƙa. Amma masu sana'ar gini Birkiloli da masu tsanen ƙwaya na fada (Dagi) kodayaushe a cikin ayyuka suke basu da wani wata takameme na gudanar da ayyukansu.




## KADARORI

Kamar yadda aka ambata a baya, kashi 70% na al'ummar Yakasai ma'aikatan gwamnati ne da wasu ƙalilan masu sana'ar hannu. Kowanne ɗan unguwa nada damar Yin sana'ar da yake so. Haka kuma, mata na gudanar da sana'o'insu a gidajensu kamar sana'ar kiwon awaki, tumaki da kiwon kaji da sauran sana'o'in hannu.

# TANTANCE MATSALOLIN DA KE ADDABAR UNGUWAR YAKASAI

Al'ummar wannan unguwa sun bayyana waɗannan matsaloli dake ci musu tuwo a ƙwarya, matsalolin su ne: Shaye-shayen miyagun ƙwayoyi, ƙarancin masu faɗa aji da rashin aikin yi.

Shan Miyagun Kwayoyi: Unguwar Yakasai na fama da matsalar shan miyagun ƙwayoyi musamman ga matasa. Lamarin na shaye-shaye yayi mutuƙar rage ƙimar unguwar a idon duniya. Ya wajaba ayi duba na tsanaki ga lamarin domin dawo da martabar unguwar.

Karancin Masu Faɗa Aji: Yawancin matsalolin dake damun unguwar ya ta'allaƙa ne kacokan ga rashin masu tsawatarwa da rashin zaurukanbayar da shawarwari da jagoranci a unguwar. Samun waɗannan zaiyi mutuƙar tasiri wajen rage miyagun halaye a cikin unguwa.

Rashin Aikin Yi: Wannan lamari ne daya daɗe yana addabar al'ummar wannan unguwa ta Yakasai. Duk inda ake da samari masu zaman banza da yawa to kuwa za ayi ta samun munanan ɗabiu, za a samu raguwar wannan kuwa idan aka samu shigowar ƙungiyoyi masu zaman kansu.

| MASALA | YIYUWAR FARUWAR MATSALA | | | TASIRIN MATSALAR | MA'AUNI | | | MATAKIN DA AKA ƊAUKA NA RAGE FARUWAR MATSALAR |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | H | M | L | | H | M | L | |
| Toshewar Magudanun Ruwa (Kwatoci) | ✓ | | | Taƙaita zirga-zirga kasuwanci da katsewar sadarwa Rushewar gidaje | ✓ | | | Unguwar batada kyawawan magudanan ruwa, yana da kyau gwamnati ta samar da ingantattun magudanan ruwa da zasu rage ambaliyar ruwa da rusau a lokacin damuna a Unguwar. |







| | | | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Karuwar mutuwar mata masu juna biyu | | ✓ | | Tsaiko saboda ƙarancin asibitoci Babban asibitin dake kusa da unguwar anyi mishi nauyi sosai Durƙusar da rayuwar matasa | | ✓ | | Akwai buƙatar gwamnati ta samar da ƙarin ɗakunan shan magani da samar da ƙwararrun ma'aikatan lafiya da kayayyakin aiki daɗi kan waɗanda ake dasu. |
| Shan miyagun Kwayoyi da daba | | ✓ | | | | ✓ | | Akwai buƙatar kamfanonin su bunƙasa ayyukansu da daukar matasan wannan unguwa. |



TANTANCE KALUBALE DA HADURRUKAN YAKASAI








## TANTANCE HAKKOKIN MATA

'Yancin mata shi ne Haƙƙoƙinda aka keɓe musamman domin mata da 'yanmata a ƙasashen duniya masu yawa.A wasu wuraren, ire-iren waɗannan Haƙƙoƙinana tabbatar da su ne ta hanyar yi musu doka da tsarin zamantakewar al'umma. A wasu wuraren kuwa, a iya cewa an yi watsi da su. Lamuran da ake dangantawa da haƙƙin mata ba a takaita su ga 'yancin yin zabe ko takaita haihuwa kaɗai ba

A arewacin Najeriya, al'ada da addini suna cigaba da taka muhimmiyar rawa a sha'anin 'yancin mata. An samu cigaba sosai a 'yancin mata musamman wajen faɗaɗa tattalin arziƙinsu da samun damar yin ilimi da kuma yadda suke shiga a dama da su a al'amuran al'umma. Duk da wannan cigaban da aka samu, har yanzu akwai ƙalubale wajen sanya su cikin al'amuran shugabancin da jin ta bakinsu yayin a ɗaukar wata matsaya kan wani al'amari da ba su mukamai da kuma ba su damar bayar da irin tasu gudummawar a sha'anin al'umma.

An sami cigaba dangane da haƙƙoƙin mata a shekarau da yawa a wannan unguwa ta Yakasai. Mata da yan mata ana basu damar su gaji filaye daga mazajensu ko iyayensu da suka rasu haka suna da damar sayan filayen idan buƙatar haka ta tashi. Unguwar Yakasai ta ƙunshi ƙananan unguwanni da dama. Sai dai mata a wannan unguwa basa shiga a dama dasu wajen sha'anin mulki da zartarwa. A unguwar Yakasai mata na gudunar da yan sana'o'insu da kasuwancinsu. Kuma sunada iko akan kuɗaɗen da suka samu a waɗannan kasuwancin. Suna amfani da Kuɗaɗen da suka tara ta hanyar sana'o'insu domin biyan buƙatunsu na yau da kullum harma kula da harkokin gida. Da yawansu suna kiwon dabbobi kamar Shanu, da Tumaki da tsuntsayen gida.

Anyi amfani da ma'aunin cobweb domin tantance haƙƙoƙin mata. Amfani da wannan ma'aunin zai sa a fahimci abubuwan da suke kawo musu cikas wajen cigaban su da kuma matsayinsu a cikin al'umma.




Ma'aunin Cobweb Na Tantance Haƙƙin Mata

| ƁANGARE | SAKAMAKO (MATA) | SAKAMAKO (MAZA) |
|---|---|---|
| Damar samun Ayyukan Yi | 2 | 2 |
| Shugabanci | 1 | 1 |
| Kuɗin Shiga | 3 | 3 |
| Kula da Gida | 2 | 1 |
| Mallakar Kadarori | 5 | 1 |
| Tsaro | 5 | 4 |
| Samun Damar Ilimi | 4 | 4 |
| Zartar da Hukunci Kan Al'amuran Al'umma | 1 | 1 |
| Damar Sarrafa Albarkatu | 5 | 2 |
| Shiga Al'amuran Al'umma | 1 | 1 |





Jadawalin na sama na nuna tazarar da ke tsakanin maza da mata a lokacin aikin tantance haƙƙoƙin mata. Abin sha'awa, akwai daidaito na kurkusa a ratar da aka samu a tsakaninsu, wanda yake nuna cewa al'ummar unguwar sun fahimci banbancin da ke tsakanin maza da mata.

A unguwar Yakasai mata suna da ta cewa a harkar shugabanci kaɗan, sannan shiga a dama dasu sha'anin al'amuran al'umma bai taka kara ya karya ba. Duk da irin ƙoƙarinsu ba a saka su wajen zartar da hukunci. Sukan shiga a dama dasu a al'amuran kasuwanci (ƙananan sana'o'i) da siyasa, amma banda harkar shugabanci.



Matan Unguwar A Wajen Tantance Haƙƙoƙin Mata

## Take Haƙƙoƙin Ɗan Adam

Duba da rijistar haƙƙin Ɗan Adam, an gano cewa an takewa mutanen unguwar Yakasai waɗannan haƙƙoƙin:

- Haƙƙin ingantacciyar lafiya
- Haƙƙin Samun Ilimi
- Haƙƙin Samun Abubuwan more Rayuwa
- Haƙƙin Samun ingantaccen Ruwan Sha

Waɗannan haƙƙoƙi nada alaƙa da matsalolin da suke damun wannan unguwa. Dangane da wadannan matsalolin da ake takewa, al'ummar wannan unguwa sun yanke cewa matsalar Shaye-shayen Miyagun Kwayoyi ingantacciyar hanya ruwa kwalbati Rashi Mafaɗa, Zauren Bayar da Shawarwari da Lalaci, da Rashin Aikin Yi, sunƙara da Karancin ruwan sha (sune manyan matsalolin da aka tauye musu kuma matsalolin sune ummul aba isin rashin cigaban wannan unguwa. Mutanen wannan unguwa basu samun ingantaccen ilimi da lafiya a sauƙaƙe saboda yawa da nauyi da akayiwa asibitocin dake kewaye dasu). Daɗin daɗawa kuma an tauye musu haƙƙin ingantacciyar lafiya saboda ƙarancin asibiti da ƙarancin ma'aikatan lafiya a ɗakunan shan maganin unguwar.





## Lissafin Haƙƙoƙin Unguwar Yakasai

| Jihar /LRP | KANO | | | KARAMAR HUKUMA | KARAYE | | GARI | | KADEMI | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Rashin cancanta/ cancanta a samu (mata, yara, talakan da ba shi da fili ko rukunin jama'ar da aka gano) | Adadin waɗanda suka cancanci su samu a yankin da aka yi shirin | | Al'amari | Abubuwan da suka haddasa | Haƙƙoƙin da aka tauye | Kundin tsarin mulki | Adadin waɗanda suka cancanci su samu damar da suke neman haƙƙinsu a farkon fara shirin | | Waɗanda nauyin yin aikin ya hau kansu | Sauran muhimman masu ruwa da tsaki |
| | Namiji | Mata | | | | | Namiji | Mata | | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 13,100 | 14,939 | Shan Miyagun Kwayoyi | Rashin Ingantaccen Shugabanci | Haƙƙin Ingantacciyar Rayuwa | Kundin tsarin mulkin Najeriya | 13,100 | 14,939 | - G/C<br>-HISBA<br>NDLEA | Kungiyoyi masu zaman kansu<br>NGOs<br>-CBOs |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 13,100 | 14,939 | Rashin masu faɗa aji Rashin zauren Shawarwari da Lalaci | Rashin Ingantaccen Shugabanci | Haƙƙin Ababan More Rayuwa | Kundin tsarin mulkin Najeriya | 13,100 | 14,939 | - Karamar Hukumar Birni<br>-DYD | Kungiyoyi masu zaman kansu -<br>NGOs |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 13,100 | 14,939 | Rashin Aikin Yi | Rashin Ingantaccen Shugabanci | Haƙƙin Kayayyakin Aiki | Kundin tsarin mulkin Najeriya | 13,100 | 14, 939 | Ma'aikatar Ayyuka da Gidaje<br>Karamar Hukumar Birni | Kungiyoyi masu zaman kansu<br>NGOs |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 13,100 | 14,939 | Karancin Tsabtaccen ruwan Sha | Rashin Ingantaccen Shugabanci | Haƙƙin Kayayyakin Aiki | Kundin tsarin mulkin Najeriya | 13,100 | 14, 939 | -Ma'aikatar Ruwa | Kungiyoyi masu zaman kansu NGOs<br>Masu taimakawa Al'umma |

## KALUBALEN **DA KE FUSKANTAR UNGUWAR YAKASAI A HALIN YANZU**

Unguwar Yakasai ɗaya ce daga cikin unguwannin a ƙaramar humukar Birni wanda a shekaru da dama ke fama da matsaloli masu ɗinbin yawa waɗanda suka haɗa da shaye-shayen miyagun ƙwayoyi, ƙarancin masu faɗa aji kan matsalar rashin aikin yi a matsayin babbar matsalar jama'ar wannan unguwa. Bayan matsalar ƙarancin tsabtaceccen ruwan sha, matsalar ilimi, ƙarancin fitilun haskaka unguwa da magudanan ruwa, unguwar na buƙatar ƙarin kayayyakin lafiya da ma'aikatan lafiya, ƙarin makarantu da tsabtaceccen ruwan sha.

An jera matsalolin wannan unguwar ta hanyar tsarin matsalar da tafi ciwa al'umma tuwo a ƙwarya a sama. Jama'ar wannan unguwar sun zaɓi matsalar shaye-shayen miyagun ƙwayoyi da rashin masu faɗa aji a matsayin matsalolin da suka fi ci musu tuwo a ƙwarya. Saboda magance su zai taimaka shawo kan matsaloli da dama harda matsalar rashin aikin yi. Wannan zai haɓaka makarantun unguwar da rage matsalar mutuwar mata masu juna biyu yayin haihuwa da raguwar taɓarɓarewar harkokin lafiyar mazauna yankin.

## SASSAUKAR HANYAR JERA MATSALOLI

| LAMBA | AL'AMARI | MATA | YARA | MAZA | ADADI | MATSAYI |
|---|---|---|---|---|---|---|
| 1 | Rashin Aikin Yi | 18 | 14 | 41 | 73 | 3rd |
| 2 | Shaye-shayen Miyagun Kwayoyi | 24 | 15 | 40 | 79 | 1st |
| 3 | Magudanan Ruwa | 0 | 07 | 12 | 19 | 7th |
| 4 | Karancin Fitilun Haskaka Unguwa | 0 | 07 | 17 | 24 | 6th |
| 5 | Karancin Ruwan Sha | 19 | O9 | 18 | 46 | 4th |
| 6 | Ilimi | 0 | 06 | 40 | 46 | 4th |
| 7 | Lafiya | 0 | 0 | 12 | 12 | 8th |
| 8 | Rashi Mafaɗa, da Zauren Bayar da Shawarwari da Lalaci | 0 | 0 | 75 | 75 | 2nd |





## AL'UMMAR YAKASAI WAJEN JEREN MATSALOLI






# TANTANCE MATSALOLI TA AMFANI DA BISHIYAR MATSALOLI




Ita wannan bishiya na taimakawa wajen faiyace matsalolin al`umma da aka binchiko. Bishiyar matsalolin tana nuna dangantakar waɗannan matsaloli da dalilan afkuwarsu da kuma illar da suke da ita. Wannan bishiyar na nuna matsalolin da kuma bada damar sanya bakin duk wanda al`amarin ya shafa wajen gano dalilan afkuwarsu inda a ƙarshe za`a magance su. Matsalar kamar yadda tushen bishiyar ya wakilta shine ƙarancin hanyoyi da kwalbatoci. Dalilan da kuma illarsu kamar yadda al`ummar unguwar Yakasai suka tattauna an siffantasu a bishiyar matsalolin da ke biye.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN UNGUWAR YAKASAI 2016



## KUNGIYOYI DA MUTANEN DA ZASU IYA TALLAFAWA UNGUWAR YAKASAI (MASU IKO DA HUKUMOMI)

| ABUBUWAN DA AKA GANO | WAƊANDA ZA SU IYA TALLAFAWA | CIBIYOYI | DALILAN BUKATU/ ZABURARWA DOMIN KAWO CANJI | MATAKIN KARFIN IKON KAWO CANJI |
|---|---|---|---|---|
| Shaye-Shayen Miyagun Kwayoyi | 1. Mai Unguwa<br>2. Shugabannin 'Yan Daba<br>3. Kwamanda A/B<br>4. Kansila<br>5. Shugaban Karamar Hukuma<br>6. Ɗan Majalisar Jiha<br>7. Dan Majalisar Tarayya<br>8. Sanata<br>9. Liman<br>10. Iyaye<br>11. Masu Taimakawa Al'umma | 1. Ƙungiyoyin Al'umma<br>2. Kungyar Ɗaliban Yakasai<br>3. NDLEA<br>4. Kungiyar Iyayen Yara<br>5.Yakasai zumunta | Cigaba / Siyasa | 1. ƙasa<br>2. ƙasa<br>3. Sama<br>4. tsaka-tsaki<br>5. tsaka-tsaki<br>6. sama<br>7. sama<br>8. sama<br>9. ƙasa<br>10. tsaka-tsaki<br>11. tsaka-tsaki |
| Faɗakarwa/ Zauren Bayar da Shawarwari | | 1. Kungiyar Cigaban Unguwar Yakasai<br>2. NPF<br>3. Hisbah<br>4. Ma'aikatar Shari'a<br>5. Sashin Bayar da shawarwari da Jagoranci ta Jiha<br>6. Karamar Hukumar Birni da Kewaye | Cigaba / Siyasa | Kamar yadda yake a sama |
| Rashin Aikin Yi | | 1.SARERA<br>2. Ma'aikatar Mata ta Jiha<br>3. Ofishin mai Bawa Gwamna Shawara akan Masu Buƙata ta Musamman<br>4. Karamar Hukumar Birni da Kewaye<br>5. Masarautar Jihar Kano<br>6. Sashin Bayar da shawarwari da Jagoranci ta Jiha<br>7. Kungiyoyi masu zaman kansu | Cigaba / Siyasa | Kamar yadda yake a sama |

Abubuwan da suka biyo baya daga bishiyar matsaloli, an yi nazarin ƙungiyoyi da mutanen da za su iya bayar da gudummawa wajen warware matsaloli. Al'ummar unguwar Yakasai sun fitar da muhimman mutanen da suke da zarafin tallafawa domin samar da canjin da ake fata a unguwar.





## MUTANE

Bayan zayyana matsalar ƙarancin hanyoyi da kwalbatoci a matsayin babbar matsalar dake damun al'ummar wannan unguwa, jama'ar unguwar sun tattauna akan wasu mutane da ƙungiyoyin da za su iya hubɓasa dangane da samar da hanyoyi da kwalbatoci saboda irin tasirin da suke da su na kawo chanji.

Al'ummar unguwar sun zayyana Gwamna da Shugaban Karamar Hukumar Birni, da Kansila, Mambobin Majalisar Jihada Mabobin Majalisar Tarayya da Sanatoci, Kwamishinan Kananan Hukumomi Mai Unguwa/Dagaci Babban limami da mutanen da zasu iya kawo canji.

## KUNGIYOYI

Dangani da ƙungiyoyi kuma, an zayyana cewa Karamar Hukumar Birni, Gwamnatin Jiha, Ma'aikatar Ayyuka da Gidaje, Ma'aikatar Kananan Hukumomi, da Kwamatin Ayyuka na Majalisar Jiha, da Masu Taimakawa Al'umma na da mutukar taka muhimmiyar rawa wajen kawo abubuwan more rayuwa a wannan unguwa.




## TANTANCE YANAYIN KARFIN IKO (NAZARI KAN WAƊANDA KEDA IKO)

An yi amfani da tsarin zane naVenn domin gudanar da wannan tantancewar. Haka kuma anyi amfani da tsarin zanen Venn domin tantance matakin ikon da wani mutum ko wata ƙungiyoyi ke da shi da kuma alaƙarsu da juna.Zanen dake tafe ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano. Sanan kuma zanen ya nuna tazarar da mutane da cibiyoyin ke dasu daga unguwar da kuma alaƙar su da juna.




KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN UNGUWAR YAKASAI 2016

Kwamitin ayyuka da gidaje na majalisar jiha nada mutaƙar tasiri da karfi wajen samar da canji dangani da gina hanyoyi da kwalbatoci waɗanda zasu haɗa unguwar da sauran unguwanni maƙota. Haka kuma yana da alaƙa da irin taimakon da Sanata da Wakilinsu na Majalisar Tarraya, Majalisar Karamar Hukuma da kuma al'ummar unguwar za su bayar. Ma'aikatar Ayyuka da Gidaje nada mutuƙar tasiri da kyakkyawar alaƙa da ma'aikatar ƙananan hukumomi da ƙaramar hukumar Birni.Itama Majalisar Zartarwa ta ƙaramar hukuma nada irin wannan tasirin.Gashi kuma Majalisar Zartarwar Karamar Hukuma ita ce take sadar da buƙatun mutane da majalisar.

Rawar da masu sarautun gargajiya da yan kishin ƙasa ke da ita ƙalilan ce gurin samar da canji duk da cewa sun fi kusa da al'umma. Suma Malaman Addini da Kansiloli irin wannan rawar sukeda ita wajen kawo canji.

| LAMBA | MATSALA | ABIN DA YA HADDASA | TASIRI | WAƊANDA SUKAFI CUTUWA |
|---|---|---|---|---|
| 1 | Yan Daba | Rashin Aikin Yi<br>Taɓarɓarewar Tarbiya | -Asarar Rayuka<br>-Asarar Dukiyoyi<br>-Rashin Tsaro | Gabaɗayan Al'umma |
| 2 | Shaye-Shayen Miyagun Kwayoyi | Rashin Aikin Yi<br>Rashin masu bayar da magunguna | -Mutuwa<br>Ciwon Hauka<br>Rashin Girmama Juna | Gabaɗayan Al'umma |
| 3 | Sace sace | - Miyagun Kwayoyi<br>Zaman Kashe wando | - | Gabaɗayan Al'umma |
| 4 | Ambaliyar Ruwa | Cushe magudanan Ruwa<br>Zubar da shara ko'ina | - Asarar Rayuka<br>-Asarar Dukiyoyi | Gabaɗayan Al'umma |










# TANTANCE HANYOYIN SAMUN BAYANAI

Unguwar Yakasai na samaun bayanai daga waje ta hanyar gidajen radio da talabijin da zantukan jama`a da wayar tarho da masu shela, yanargizo, makarantu da sauran wajen tarukan addini a wannan unguwa.Wasu lokutan waɗannan bayanai ana faɗarsu lokacin bukukuwan ɗaurin aure ko raɗin suna.

Amfani da wayar Salula da batutuwan al'umma hanyoyi ne da jama'ar wannan unguwa ke musayar bayani da jama'ar wasu unguwannin. Dagaci da masu sarautun gargajiya sune masu magana da yawun mutanen wannan unguwa.



# TSARIN DA AKA SHIRYA GUDANARWA NA AL`UMAR UNGUWAR YAKASAI

A ƙarshen tattaunawar, an fitar da ƙwaƙƙwaran tsarin da za a bi domin warware matsalolin da aka gano ta hanyar samar da wani kwamiti wanda zasu haɗa ƙarfi da ƙarfe da CITAD domin magance abubuwan da ke ci wa al'ummar unguwarYakasai tuwo a ƙwarya. Al`umar unguwarYakasai sun binciko tare da gwada mizanin gazawar dake faruwa aunguwar. An kuma yi amfani da wani teburin auna gazawa wajen tattauna waɗannan batutuwa.Jadawalin da ke biye tsari ne na ayyukan da za aiwatar domin ganin mafarkin unguwar ya zama gaskiya na ganin an samar da hanyoyi da kwalbatoci waɗanda zasu haɗa unguwar Yakasai da sauran unguwanni.








# TSARIN DA AKA SHIRYA GUDANARWA NA AL`UMAR UNGUWAR YAKASAI

| MAHIMMAN BATUTUWA | AIKIN DA AKA TSARA GUDANARWA | WAƊANDA SUKA ƊAUKI NAUYI | KAYAN AIKIN DA AKE BUKATA | MATSALOLI | SHAIDAR SAMUN NASARA | TSAWON LOKACI |
|---|---|---|---|---|---|---|
| Rangadi don saduwa da sauran jama`a a unguwar Yakasai | Ganawar Baka-da-Baka Kiran Waya da Ganawa Samar da kwamiti | Kwamitin samar da kundin Cigaban na Unguwar | Bayani game da wannan shiri samar da rukunin Al'umma | Zirga-zirga Kuɗin waya | Rahoto | Sati Biyar (29/2/2016) |
| Daftarin cigaban unguwar Yakasai | Gabatarwa da amsar bayanai | CITAD/ Jami`in Unguwar | Albarkatun Dan`adam | Karancin lokaci Da Kayan aiki | Kammalallen daftarin cigaban unguwar | May 2016 |
| Kaddamar da Kundin Cigaban unguwar Yakasai | Raba wasiƙun gaiyata - Haɗa gwiwa da kafafan yaɗa labarai -tsara taro | CITAD/ Jami`in Unguwar | Tuntuba Al'ummar gari Wasiƙu Sufuri Yaɗa saƙon a kafafen watsa Labarai | Lokaci | Kaddamar da Kundin Cigaban unguwar Yakasai | |
| Ziyara domin samun mai gudanar da Aiki | Ziyarce-ziyarce | CITAD/ Jami`in Unguwar | Jama'ar gari littafin Unguwa -kafar yaɗa Labarair | Lokaci | Sabgogi | |